Littafi mai Tsarki na yara
Ke gabatar da



# Yarinyar da ta Rayu sau Biyu

Wanda ya Rubuta: Edward Hughes

Mai Zane: Janie Forest
Alastair Paterson

Mai niyyan daukan nauyi: Ruth Klassen

Fassarawa: Bible Society Nigeria

Wanda ya Wallafa: Bible for Children
www.M1914.org

©2023 Bible for Children, Inc.
Zaku iya kofan wanna labarin ku wallafa idan
har ba zaku sayar da shi.

Yayirus wani shugaban addinin Yahudawa ne wanda ya bauta wa Allah ya kuma koyar da Kalmar allah wa wadansu. Wata rana, wani mummunar damuwa ta zo wa Yayirus. Kaunattaccen ‘yarsa, mai shekara goma sha biyu ta yi rashin lafiya. Ya zama babu wani wanda zai iya taimaka mata. Mummunan ciwo ne. Yayirus ya sani tabas yarinyar tana mutuwa ne.



Mutum daya ne kadai wanda zai iya taimaka wa ‘yar Yayirus. Yayirus ya fita neman inda zai same Yesu domin ya kawo shi gidansa. Yayirus ya sani cewa abokansa na addini ba su yarda da Yesu ba.



Amma Yayirus bai damu ba. Dole ne ya nemi taimako da sauri kafin ‘yarsa ta mutu.

Yayirus ya same Yesu kewaye da mutane.



Ya durkusa a kafan Yesu. “‘Yar karamar ‘ya ta tana kwanciye kusa da mutuwa,” yana roko cikin hanzari. “Zo ka sa hannu a kanta domin ta warke, ta kuma rayu.”



Yesu ya tafi tare da Yayirus. Amma ba su iya yin tafiya da sauri ba saboda yawan mutane. Akwai wata wanda ta yi shekara goma sha biyu tana ciwo. Ta je wuraren likitoci duka (ta kashe duka kudinta) babu taimako. Oh, ina misalin marmarin ta ga Yesu!



**Mene ne macen nan za ta yi? "Da kawai zan iya taba kyalen rigarsa, zan warke," tana gaya wa kanta. Sai ta yi ta matsawa kusa da Yesu. Sa'an nan, ta mika hannunta, sai ta taba rigar Yesu.**



A bin al'ajibi!  A bin AL"AJIBI!  Macen ta warke. Nan take!  Gaba ki daya!  Ta sani cewa ta warke cike da karfin jiki gaba ki daya. Amma sai wata murya ta yi magana.  "Wane ne ya taba Ni?"  Yesu ya tambaya. Dumbun mutane sun tattaba shi.  Amma macen da ta warke ta sani cewa yana so ta fada masa game da warkewan ne. Cikin rawar jiki, sai ta gaya masa duka labarinta.

A wurin, sai ga ‘yan hidima daga gidan Yayirus. Da ganin fuskokinsu sai aka gane irin labarin bakin cikin da suke da shi kafin su yi magana. “‘Yarka ta mutu!” suka gaya wa Yayirus. Mutuwa! Kome ya yi leti. Watakila da macen nan ba ta bata wa Yesu lokaci ba… watakila, da… Mutuwa! ‘Kyakkyawar yar bebi na Yayirus ta tafi.



Sa'ad da Yesu ya ji, sai ya amsa, "Kada ka ji tsoro; ka ba da gaskiya kawai, kuma za ta warke." Wannan abu ne mai wuyan amincewa kuma ya zama da wuya ga Yayirus ya gaskata da abin da Yesu ya fada masa. 'Yarsa ta riga ta mutu.





A gidan, kowa yana kuka da makoki wa yarinyar. “Ba ta mutu ba, amma barci take yi,” Yesu ya gaya musu. Suka yi masa dariya. Sun sani cewa yarinyar ta mutu.



Yesu ya sa suka fita waje duka, ya kama yarinyar a hannu ya ce “Yar karamar yarinya, ki tashi.” Yayirus yana a wurin. Matarsa tana a wurin. Almajirai uku na Yesu suna a wurin. Dukansu sun ji kalmomin Yesu. Ko ‘yar karamar yarinyar za ta ji kalmomin, ita ma?



Matacen yarinyar ta ji umarnin Yesu! Ruhun ta ya dawo, sai ta tashi nan da nan.  Yesu ya tayar da ita daga matattu.



**Iyayen yarinyar suka yi mamaki. Yesu ya gaya musu su ba yarinyar wani abu ta ci. Ina misalin farin cikinsu; yadda suka gode wa Yesu. Kaunarsa marar iyaka da ikonsa ya dawo musu da 'yarsu daga matattu.**



# Yarinyar da ta Rayu sau Biyu

Tahiri da ga maganar Allah, littafi mai Tsarki

a na samu a

Markus 5, Luka 8

"Shigowar maganar ka yana baduar kawo haske." Zabura 119:130

# KARSHE

**Wanan tahiri daga littafi mai-tsarki na mana bayanin Allah mu wanda ya halicce mu wanda yake son mu san shi.**

**Allah ya san da cewa mun yi abubuwan da ba su da kyau, wanda yake kira zunubi. Sakamakon zunubi mutuwa ne, amma Allah ya na kaunan mu sosai. Ya aiko da Ɗansa Yesu, ya mutu a kan giciye ya sha wahala domin zunuban mu. Kuma sai Yesu ya tashi daga matattu ya koma gida a sama. Idan ka bada gaskiya ga Yesu. Ka roƙeshi gafaran zunuban ka, zai yafe. Kuma zai zo ya zauna a cikin zuciyan ka kaima kuma zaka zauna a zuciyar shi har abada.**

**Idan ka yadda da wannan gaskiya ne, Ka cewa Allah:**
**Ya Yesu, na bada gaskiya kai Allah ne, ka kuma zamu mutum don ka mutu domin zunubi na, kuma yanzu ka tashi. Ina roƙon ka, ka shiga cikin zuciya na kuma ka yafe min zunubai na, Domin in samu sabon rai yanzu, kuma wata rana in zauna tare da kai har abada. Ka taimake ni in yi maka biyayya kuma in yi rayuwan da zai gamshe ka a matsayin ɗan ka. Amin.**

**Ka karanta littafi mai-tsarki kuma ka yi magana da Allah a kulla yaumin. Yahaya 3:16**